MACE A MAHANGAR AL'ADA

Muhammad Rabi'u TAHIR
Sashen Harsuna da Al'adun Afirka
Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria

1.0 Gabatarwa

Mace wata halitta ce wadda Allah ya yi wa daraja da ɗaukaka a cikin jinsin al'umma,domin ta zama abokiyar zama da sutura a tsakani,sannan take da wani matsayi da kula a mahaliin uwa ko mata ko 'ya da sauransu.(Al-Hashimi, 2013) Wannan ya nuna kenan mace wata sinadari ce wadda al'umma ba ta iya ginuwa sai da ita wajen samar da zuri'a ta gari da ɗawainiyar tarbiyya har zuwa girma.

Saboda haka al'adar Hausawa ta ba mace mahalli a kusan kowane nau'i nata, domin haka haka ne take hangen mace a matakai na rayuwa da dama, a wani ɓangaren a matsayin uwa ko abokiyar zama ko 'ya ko mai gina al'umma da sauransu. Wannan yasa idan an duba tun daga wasan 'yar tsana wanda yake kandamin wasa ne,za a ga ya ƙunshi rayuwar 'ya mace a matsayin uwa da kuma 'ya a mahangar al'ada tun daga tsumman goyo har zuwa aure. Sannan habarcen tatsuniya shi ma kusan babu wani gurbi da ya bari face sai an ga wani abu na koya tarbiyya a habarcen daga mace a matsayin abokiyar zama ko 'ya ko uwa. Haka kuma habarce rubutacce nan ma an ce wani abu dangane da 'ya mace. Haka waƙa nan ma an nuna wani abu danganeda inganta rayuwa ga mace, da kuma yadda al'ada take hango mace a uwa tagari mai nuni da kuma ci gaban al'umma.

Hausawa na ɗaukar tarbiyya wani babban masaki wanda yake kai al'umma tudun-mun-tsira a rayuwa, kuma da ita ne al'umma ke zama abin alfahari da kwatance domin a yi koyi da ita.

Tarbiyya harka ce wadda kusan kowa a cikin al'umma yake ba da tasa gudummawa gwargwadon matsayinsa da kuma yanayin shekaru ko kuma muƙami da dangantakar mutum. Da haka ne ake iya cewa al'umma na iya zama jami'an tarbiyya a cikin al'ummarsu. Sai dai haka ba yana nufin tarbiyya an barta kara-zube ba ne, akwai tsari dangane da yadda kowa ke iya ba da tashi gudummawar, tun daga iyaye har zuwa sauran al'umma (Umar, 1987).

Shi kuwa adabi tabarau ne da kullum yake leƙawa, ya gano matsalolin da suke faruwa a tsakanin al'ummarsa, ko suke dabaibaye da al'amuran rayuwa na wannan al'umma, domin samun damar yin tsokaci. Domin harkoki irin na 'ya mace da auratayya da na maƙwabtaka da tarbiyyar yara duk suna da babban tasiri a al'adar Hausawa (Tahir, 2013).

2.0 Mace

Allah Ya halicci mace ta zama sutura ga namiji, haka shi ma ya zama sutura ga mace, duk da cewa mata suna da rauni da kuma ƙarancin hankali da tunani, wanda hakan bai hana a hana su haƙƙinsu kamar yadda wanda Ya halicce su Ya nuna a yi, sannan ƙirar jikin mace yana da tsari na musamman, wanda hakan ya bambanta ta domin ta kebanta da wasu ayyuka, irin waɗanda suka dace da yanayin jikinta da kuma hankalinta (Jamal, 2005) .

Ko da yake a al'adar Hausawa mace tana yin karatu kamar yadda namiji yake yi, sai dai kowa matsayinsa ya bambanta, sannan mace a wurin Bahaushe kafin addini a iya cewa kusan da ita ake gudanar da ayyukan yau da kullum, musamman aikin gona da itace, sannan

ta dawo ta yi aikin gida, wannan ya nuna kenan mace tana ba da tata gudummawa gwargwadon raunin da ake gani take da shi a cikin al'umma(Tahir, 2012) .

Wasu masana suna hangen 'ya mace a wata mahanga ta dauri, wadda suke fahimtar mace ba ta da wata ƙima ta azo a gani. Wasu kuwa irin su Muhammad. (2013) da Jamal (2005) da Rabi (2009) suna ganin cewa 'ya mace ita ce al'umma domin da ita ce kusan tubalin da ake gina al'umma da ita, sannan kuma ita ce kanwa uwar gami a kowane irin muhalli na al'adun al'ummar Hausawa.

Mace kafin addini ba ta wuce wani kayan more rayuwa ba da biyan buƙata. Domin ana iya mallakarta kamar yadda ake iya mallakar kowane abu na ƙawa, kamar riga ko abin hawa da sauransu. Irin wannan rashin ƙima har ya kai namiji na iya auren adadin da yake buƙata ba tare da wata ƙa'ida ba, ko kuma a gade ta har sai in ta fanshi kanta daga magadan miji. Amma an mayar da su kamar wasu jakuna. Ba su da wata ƙima, face a biya buƙatar sha'awa da su, sannan su je su tsare aikin gida da na gona (Dunfawa, 2004: Juz'i na 1, 137-138) .

Haka kuma mace ba ta da wata ƙima ta a zo a gani a cikin wasu al'umma kamar da namiji. Domin komai daɗewa za ta bar gidansu zuwa gidan wani, domin samun nata iyalin, sannan kuma idan an dubi tsarin shugabanci ai mace ba ta za ma sarki bare ta shugabanci al'umma, idan an yi la'akari da tsarinta kamar mai zuwa ce da komawa, wannan ne ya sa wasu da yawa daga cikin jama'a ba sa sanya mace a matsayin zuri'arsu, dalili a wurin su ai ta koma mallakar wani da kuma iyalin wasu jama'a saɓanin jama'ar da ta fito (Halima, 2008: Juz'i na 2. 185-189) .

Mace a adabi tamkar kanwa uwar gami ce, ganin yadda suke taka muhimmiyar rawa a wannan fanni. Hasali ma abu ne mai wuya a ce an tsara wani habarce na baka ko rubutacce ko wasan kwaikwaiyo ba tare da mace ta zama wata ginshiƙi daga cikin taurari ba. Da kuma irirn matsayinsu a dangane da yadda suke zama tubali wajen gina rayuwar al'umma (Rabi, 2009: juz. na 3 : 50) .

Saboda haka adabi bai ƙyale al'umma kara-zube ba, a'a ya zama jini da tsoka tsakanin sa da al'ummar da yake tattare da ita. Da haka ne ɗabi'un al'umma ke bayyana ta hanyar habarcensu na baka ko kuma rubutacce, ko kuma ta hanyar habarcen tatsuniya ko na labari ko na tarihihi ko na almara ko wasan kwaikwayo ko waƙa da sauransu. Duk waɗannan hanyoyi ne waɗanda idan aka ɗauki ɗaya daga ciki, a iya tantance wani abu dangane da halayyar wani jinsi a cikin wannan al'umma.

Mace na ɗaya daga cikin jinsin da Hausawa suke girmamawa da kuma martabawaa kusan kowane nau'i na adabin Hausawa, musamman saboda gudummawar da take bayarwa wajen gina rayuwar wannan al'umma ta fuskoki da dama. Duk da irin wannan gudummawa da take bayarwa, wani lokaci akan sami akasi, ta yadda ake iya fito da wasu halaye da ɗabi'u dangane da yadda ake zamantakewa da ita a cikin al'umma (Laurie, 1998:58).

2.1wasan 'Yar Tsana

Wasan 'yar tsana wasa ne da ya ƙunshi yara ƙanana, waɗanda suke aiwatar da shi domin nishaɗi a tsakaninsu da sauran yara. Tun asali Hausawa suna da wasan 'yar tsana ko 'yar ƙashi, wanda suka ƙirƙiro shi da kansu, domin nishaɗi da nusarwa. Saboda haka wasan 'yar tsana ya ginu a dalilin gargajiya da al'adar rayuwar Hausawa. Da haka ne wasan ya kusan zama ko'ina an san shi ko an taɓa yi a lokacin ana yara.

Har ila yau, wasan 'yar tsana na yara mata ne. Su 'yan matan za su sami ƙashi su shirya shi kamar wata yarinya. Wannan ƙashin za a yi ta reno tun daga haihuwa ya zuwa lokacin da za a yi 'mata' aure.A wannan lokacin har goro da demun minti ake rabawa domin

gayyata ga sauran 'yan mata 'yanuwanta. A irin wannan wasan ana kwaikwayon yadda ake gudanar da halin rayuwa. A lokacin za a reni yarinyar, a koya mata tarbiyya da duk wasu halayen kirki da ake so ta koya (Ahmad, 1990).

Kamar yadda bayani ya nuna cewa yara mata ke aiwatar da wasan 'yar tsana, da nufin koyon halin rayuwa da tarbiyya da nishadi. Wannan ya nuna idan har za a koyi tarbiyya tun daga kuruciyar 'ya mace, an fara samun tubalin gina tarbiyyar wannan yarinyar tun daga wasan 'yar tsana.

Bikin 'yar tsana yara mata su ne suke yin sa; yarinya, idan ta mallaki 'yar tsana, sai ta rika yi mata renon yarinya ta gaske, ta dinga kwaikwayon ciyar da ita, tana yi mata wanka. Idan ta girma, ta yi mata kunshi da ado na tufafi wanda teloli suka dinka da kyallaye. A kwana a tashi sai ta ce ita yarinyarta ta isa aure, sai ta raba wa kawayenta goro da alewa, ta gaya musu ranar biki. Sai ta tanadi kananan kwanuka da tasoshi, har ma da dan gado, matasan kai, da kumbuna ko kobot. Su kuma kawaye su zo ranarkamu, su suffanta duk abubuwan da manya suke yi na bukukuwan aure tun daga ranar kamu har su kunshi da tarewa. Sukan kawo kudin gudummawa wurin uwar 'ya.(Yahaya, 1978)

Saboda haka wasan 'yar tsana wasa ne, da ya kunshi kananan yara mata, wanda yake da lafazi kusan nau'i biyu, na manya da kuma lafazin yara 'yanwasan. Akan sami kan rake ko kashi, sai a maida shi kamar 'ya ta gaske, za a raine ta da kuma ba ta tarbiyya kamar yadda yaran suka gani a wajen iyayensu, za a kai ga yaye da kuma koya mata sauran abubuwan kamar sanya tufafi da kwalliya da kuma iya magana yadda ya dace, har zuwa lokacin aure. Daga nan ne za a raba goro a gayyaci makwabta yara su zo domin a aiwatar da sha'anin biki, har zuwa gidan miji kamar tarewa da yi mata fada, ta yadda za ta zauna da miji lafiya da kuma sauran makwabta.

2.3 Mace a Wasan 'Yar Tsana

Wasan 'yar tsana harshe ne wanda yake mai tafiya da yadda manya suke a wannan lokaci, wanda ya kunshi iyaye da kuma mai gida,lafazinsu lafazi ne na iyaye, duk da karin murya irin na manya, wani lokaci za a ji mai gida yana yi ma iyalinsa fada, musamman idan sun yi wani abu ba daidai ba, wani loto kuma harshen wasan yana magana kwatankwacin yadda zama yake a tsakanin iyaye da 'ya'yansu, sau da yawa za a fahimci yara sun raba gidan wasan 'yar tsana zuwa gida biyu, da gidan da ake aiwatar da wasan ya hada da uwa da 'ya da mai gida, sannan makwabta wadanda su ne ake gayyata wajen bikin 'yar tsana. Haka kuma lafazin wasan yana hada lafazin yara da kuma na manya dangane da yadda wasan yake tafiya, har lokacin da za aurar da 'yar tsana.

Haihuwa wata hanya ce ta samun zuriya mai kyau, a wasan 'yar tsana yara kan fara kula da cikin haihuwa tun daga lokacin da wasan ya fara kankama. Sai su fara nuna wa mai ciki ga yadda za ta yi wajen kula da abin da ke cikinta, ta nuna shan wadansu jike-jike a wasance, da kuma fadakar da ita nauyin da ke kanta na kula da cikin kafin tahaihu.

Uwa a wasan 'yar tsana tana fara kula da yarinyarta ne tun daga lokacin da ta haifi yarinyar. Wani lokaci ma uwar kan yi kokarin ba yarinyar abinci da koya zama da rarrafe da sauran zantukan yau da kullum, duk haka yana faruwa ne a yayin da ake cikin gudanar da wasa.

An shiga mataki na gaba wajen gina tarbiyya a wasan, daga wannan lokai ne ake fara koya wa yarinyar sanya kaya ko tufafi. Da kuma nuna wa 'yar yadda ake yin tsarki da wasu hidindimu, kamar fahimtar jama'ar gida tun daga ita kanta uwa da kuma sauran makwabta, sannan a wannan lokaci ne za afara nuna mata wasu halaye kamar ladabi da biyayya, a kuma fara nuna mata ado kamar yi mata kunshi da tufafi da sauransu.

ta dawo ta yi aikin gida, wannan ya nuna kenan mace tana ba da tata gudummawa gwargwadon raunin da ake gani take da shi a cikin al'umma(Tahir, 2012) .

Wasu masana suna hangen 'ya mace a wata mahanga ta dauri, wadda suke fahimtar mace ba ta da wata kima ta azo a gani. Wasu kuwa irin su Muhammad. (2013) da Jamal (2005) da Rabi (2009) suna ganin cewa 'ya mace ita ce al'umma domin da ita ce kusan tubalin da ake gina al'umma da ita, sannan kuma ita ce kanwa uwar gami a kowane irin muhalli na al'adun al'ummar Hausawa.

Mace kafin addini ba ta wuce wani kayan more rayuwa ba da biyan bukata. Domin ana iya mallakarta kamar yadda ake iya mallakar kowane abu na kawa, kamar riga ko abin hawa da sauransu. Irin wannan rashin kima har ya kai namiji na iya auren adadin da yake bukata ba tare da wata ka'ida ba, ko kuma a gade ta har sai in ta fanshi kanta daga magadan miji. Amma an mayar da su kamar wasu jakuna. Ba su da wata kima, face a biya bukatar sha'awa da su, sannan su je su tsare aikin gida da na gona (Dunfawa, 2004: Juz'i na 1, 137-138) .

Haka kuma mace ba ta da wata kima ta a zo a gani a cikin wasu al'umma kamar da namiji. Domin komai dadewa za ta bar gidansu zuwa gidan wani, domin samun nata iyalin, sannan kuma idan an dubi tsarin shugabanci ai mace ba ta za ma sarki bare ta shugabanci al'umma, idan an yi la'akari da tsarinta kamar mai zuwa ce da komawa, wannan ne ya sa wasu da yawa daga cikin jama'a ba sa sanya mace a matsayin zuri'arsu, dalili a wurin su ai ta koma mallakar wani da kuma iyalin wasu jama'a saboanin jama'ar da ta fito (Halima, 2008: Juz'i na 2. 185-189) .

Mace a adabi tamkar kanwa uwar gami ce, ganin yadda suke taka muhimmiyar rawa a wannan fanni. Hasali ma abu ne mai wuya a ce an tsara wani habarce na baka ko rubutacce ko wasan kwaikwaiyo ba tare da mace ta zama wata ginshiki daga cikin taurari ba. Da kuma irirn matsayinsu a dangane da yadda suke zama tubali wajen gina rayuwar al'umma (Rabi, 2009: juz. na 3 : 50) .

Saboda haka adabi bai kyale al'umma kara-zube ba, a'a ya zama jini da tsoka tsakanin sa da al'ummar da yake tattare da ita. Da haka ne dabi'un al'umma ke bayyana ta hanyar habarcensu na baka ko kuma rubutacce, ko kuma ta hanyar habarcen tatsuniya ko na labari ko na tarihihi ko na almara ko wasan kwaikwayo ko waka da sauransu. Duk wadannan hanyoyi ne wadanda idan aka dauki daya daga ciki, a iya tantance wani abu dangane da halayyar wani jinsi a cikin wannan al'umma.

Mace na daya daga cikin jinsin da Hausawa suke girmamawa da kuma martabawaa kusan kowane nau'i na adabin Hausawa, musamman saboda gudummawar da take bayarwa wajen gina rayuwar wannan al'umma ta fuskoki da dama. Duk da irin wannan gudummawa da take bayarwa, wani lokaci akan sami akasi, ta yadda ake iya fito da wasu halaye da dabi'u dangane da yadda ake zamantakewa da ita a cikin al'umma (Laurie, 1998:58).

2.1wasan 'Yar Tsana

Wasan 'yar tsana wasa ne da ya kunshi yara kanana, wadanda suke aiwatar da shi domin nishadi a tsakaninsu da sauran yara. Tun asali Hausawa suna da wasan 'yar tsana ko 'yar kashi, wanda suka kirkiro shi da kansu, domin nishadi da nusarwa. Saboda haka wasan 'yar tsana ya ginu a dalilin gargajiya da al'adar rayuwar Hausawa. Da haka ne wasan ya kusan zama ko'ina an san shi ko an taba yi a lokacin ana yara.

Har ila yau, wasan 'yar tsana na yara mata ne. Su 'yan matan za su sami kashi su shirya shi kamar wata yarinya. Wannan kashin za a yi ta reno tun daga haihuwa ya zuwa lokacin da za a yi 'mata' aure.A wannan lokacin har goro da deman minti ake rabawa domin

gayyata ga sauran 'yan mata 'yanuwanta. A irin wannan wasan ana kwaikwayon yadda ake gudanar da halin rayuwa. A lokacin za a reni yarinyar, a koya mata tarbiyya da duk wasu halayen kirki da ake so ta koya (Ahmad, 1990).

Kamar yadda bayani ya nuna cewa yara mata ke aiwatar da wasan 'yar tsana, da nufin koyon halin rayuwa da tarbiyya da nishadi. Wannan ya nuna idan har za a koyi tarbiyya tun daga kuruciyar 'ya mace, an fara samun tubalin gina tarbiyyar wannan yarinyar tun daga wasan 'yar tsana.

Bikin 'yar tsana yara mata su ne suke yin sa; yarinya, idan ta mallaki 'yar tsana, sai ta rika yi mata renon yarinya ta gaske, ta dinga kwaikwayon ciyar da ita, tana yi mata wanka. Idan ta girma, ta yi mata kunshi da ado na tufafi wanda teloli suka dinka da kyallaye. A kwana a tashi sai ta ce ita yarinyarta ta isa aure, sai ta raba wa kawayenta goro da alewa, ta gaya musu ranar biki. Sai ta tanadi kananan kwanuka da tasoshi, har ma da dan gado, matasan kai, da kumbuna ko kobot. Su kuma kawaye su zo ranarkamu, su suffanta duk abubuwan da manya suke yi na bukukuwan aure tun daga ranar kamu har su kunshi da tarewa. Sukan kawo kudin gudummawa wurin uwar 'ya.(Yahaya, 1978)

Saboda haka wasan 'yar tsana wasa ne, da ya kunshi kananan yara mata, wanda yake da lafazi kusan nau'i biyu, na manya da kuma lafazin yara 'yanwasan. Akan sami kan rake ko kashi, sai a maida shi kamar 'ya ta gaske, za a raine ta da kuma ba ta tarbiyya kamar yadda yaran suka gani a wajen iyayensu, za a kai ga yaye da kuma koya mata sauran abubuwan kamar sanya tufafi da kwalliya da kuma iya magana yadda ya dace, har zuwa lokacin aure. Daga nan ne za a raba goro a gayyaci makwabta yara su zo domin a aiwatar da sha'anin biki, har zuwa gidan miji kamar tarewa da yi mata fada, ta yadda za ta zauna da miji lafiya da kuma sauran makwabta.

2.3 Mace a Wasan 'Yar Tsana

Wasan 'yar tsana harshe ne wanda yake mai tafiya da yadda manya suke a wannan lokaci, wanda ya kunshi iyaye da kuma mai gida,lafazinsu lafazi ne na iyaye, duk da karin murya irin na manya, wani lokaci za a ji mai gida yana yi ma iyalinsa fada, musamman idan sun yi wani abu ba daidai ba, wani loto kuma harshen wasan yana magana kwatankwacin yadda zama yake a tsakanin iyaye da 'ya'yansu, sau da yawa za a fahimci yara sun raba gidan wasan 'yar tsana zuwa gida biyu, da gidan da ake aiwatar da wasan ya hada da uwa da 'ya da mai gida, sannan makwabta wadanda su ne ake gayyata wajen bikin 'yar tsana. Haka kuma lafazin wasan yana hada lafazin yara da kuma na manya dangane da yadda wasan yake tafiya, har lokacin da za aurar da 'yar tsana.

Haihuwa wata hanya ce ta samun zuriya mai kyau, a wasan 'yar tsana yara kan fara kula da cikin haihuwa tun daga lokacin da wasan ya fara kankama. Sai su fara nuna wa mai ciki ga yadda za ta yi wajen kula da abin da ke cikinta, ta nuna shan wadansu jike-jike a wasance, da kuma fadakar da ita nauyin da ke kanta na kula da cikin kafin tahaihu.

Uwa a wasan 'yar tsana tana fara kula da yarinyarta ne tun daga lokacin da ta haifi yarinyar. Wani lokaci ma uwar kan yi kokarin ba yarinyar abinci da koya zama da rarrafe da sauran zantukan yau da kullum, duk haka yana faruwa ne a yayin da ake cikin gudanar da wasa.

An shiga mataki na gaba wajen gina tarbiyya a wasan, daga wannan lokai ne ake fara koya wa yarinyar sanya kaya ko tufafi. Da kuma nuna wa 'yar yadda ake yin tsarki da wasu hidindimu, kamar fahimtar jama'ar gida tun daga ita kanta uwa da kuma sauran makwabta, sannan a wannan lokaci ne za afara nuna mata wasu halaye kamar ladabi da biyayya, a kuma fara nuna mata ado kamar yi mata kunshi da tufafi da sauransu.

A lokacin da yarinya ta kai budurwa a wasan 'yar tsana sai ka ga ana shirye-shiryen koya mata wasu halaye na alkunya da juriya da kuma nuna karamci da sauran kyawawan ɗabi'u, sannan ana koya mata guje wa munanan halaye da kuma yadda ake zama da jama'a. Haka kuma a wannan lokacin ne ake fara shirya biki, za a tanaji 'yan kwanoni da tasoshi da gado. Daga nan sai a raba goron gayya zuwa ga ƙawaye, har zuwa lokacin da za a kai ga biki, za a yi biki kamar yadda manya ke yi wadanda suka haɗa da sa lallae da tarewa da sauran al'amuran aure.

3.0 Habarcen Tatsuniya

Habarce kalma ce da Hausawa suka aro daga Larabci wadda ake kira 'al-khabar' watau labari. Sai suka Hausantar da wannan kalma da suna habarce a matsayin labari na baka ko rubutacce, labarin nan na iya kasancewa tatsuniya ce ko kuwa tarihi ne ko tarihihi ko ƙissa ko hikaya da sauransu.

'Khabar' labari ko sabon labari, labarin duniya idan mutum biyu suka haɗu abu na farko da suke fara tambaya, shi ne labarin duniya ko kuma na ji labarinka, ko kuma ka ba da labari **'haberta'**.(Robinson, 1913: Vol.1. P-226.)

Masana da dama sun haɗu a ra'ayi ɗaya dangane da habarcen tatsuniya yana da lokaci na musamman da mahalli da kuma masu sauraro wadanda basu wuce yara ba. Ga misali, masana irin su Gusau, (2000) da Ahmad, (1997) da Bichi, (1979) da Junaiɗu, (1990) da Skinner, (1980) da Yahaya, (1979) sun yi ittifaki cewa tana da mabudi da kuma marufi, kafin a fara da kuma bayan an gama.

Idan aka yi la'akari da bayanin da aka gabatar, ya nuna kenan wadannan mabudai da marufi, alamu ne da ke nuna yadda ake jawo hankalin mai sauraro, da nufin sauraron wani ilimi da zai taimaka masa wajen harkokin yau da gobe na rayuwa, da kuma sanin hanyoyin da zai bi wajen warware matsalolin rayuwa.

3.1Mace a Habarce

Duk da cewa mata na taka muhimmiyar rawa a al'amuran rayuwa na jama'a, wannan baya hana habarce ya fito da wasu ɗabi'u ko halaye wadanda mata ke nuna wa dangane da irin matasyin da suke da shi a kowane irin yanayi. Domin wani lokaci habarce kan nuna halin matar uba ga 'ya'yan miji ko kuma halin mace tsakaninta da kishiyoyinta ko kuma wata ɗabi'a tsakanin 'yan mata da sauransu.

Habarcen tatsuniya bai zama koma-baya ba, wajen nuna yadda mace take wajen gina al'umma da kuma yadda take inganta rayuwar al'umma, idan aka dubi mace irin su ƙoƙi matar gizo, yadda ta zama tubali wajen gina rayuwa; ƙoƙi kawai na iya zama jigo a fagen habarcen tatsuniya kasancewarta tubali wajen gina al'ada da kuma saita tunanin al'umma.
misali:

Tatsuniyar gizo da budurwar danko , wannan tatsuniya ce wadda take ɗauke da biyayya da haɗin-kai, sannan ga nuna haƙuri da girmama abokin zama dangane da neman na kai wajen aikin gonar gizo, haka kuma babu nuna wani gazawa musamman daga gizo a lokacin da yake aiwatar da hikimominsa a gida da kuma waje. (Yahaya, 1974: sh-1-2)

Saboda haka daga habarcen da aka gabatar, za a fahimci cewa ƙoƙi tana koyar da 'ya mace al'adar yadda ake kyautata danganta a tsakani abokin zama, idan an kalli yadda ƙoƙi ke nuna biyayya ga maigida gizo, a kowane lokaci yake neman haɗin kai yana samu, baya ga biyayya ga nuna haƙuri dangane da halayyar maigidanta, da kuma ba shi shawara. Duk

wadannan koki tana kokarin gina 'ya mace ne yadda ake zamantakewa da abokin zama a duk lokacin da aka sami kai a wani matsayi mai dadi ko akasin haka.

Domin daga habarcen za a fahimci gizo yana nuna wayo ne, saboda yana bukatar cin gyada, amma duk da halinsa da ta sani bai sa ta ki bas hi gyadar ba saboda matsayinsa na mai gidanta, da kuma ba shi hadin kai domin cim ma nasara ga al'amuransa na yau da kullum.

Wannan muhimmin tubali ne na gina rayuwar 'ya mace wajen iya rayuwa mai inganci tare da abokin zama, domin idan mace ba ta ba maigida hadin kai kamar yadda koki take ba maigidanta ba, da wuya a sami ci gaba a wannan al'umma, domin da haka ne sauran mata a wannan gida za su fahimci yadda ake gina rayuwa mai nagarta.

Tatsuniyar gizo ita ce wadda gizo ya fito a matsayin tauraro da matarsa koki bi-yarima, wani lokaci yana taka rawa iri biyu , domin wani lokaci yakan fito mutum mai son kansa, maras son taimakon wani, in ma an yi masa rana, to shi fa dare zai yi.....(Gusau,2000: sh-16-17)

A wannan habarce an nuna zaman iyali a tsakanin mace da maigidanta, wanda ita ce mace tamgar da dubu, domin ban da wannan habarcen babu wani habarce wanda ya nuna in da gizo ya taba yin amarya, domin a nuna yadda ake gina ko karfafa mai gida, koki ba ta nuna wata damuwa ba dangane da amaryar da gizo ya yi. Koki ta nuna biyayya da girmama namiji wajen ba shi hadin kai, da kuma rashin nuna kyama ga duk wata shawara da zai kawo, sannan da kokarin nuna masa hanaya domin cim ma nasara.

A iya cewa koki kusan ita ce kanwa uwar gami wajen kai gizo ga duk wata nasara da yake samu a kusan kowane habarce, saboda kyakkyawan tubalin da take dora masa domin ya hau wajen gudanar da al'amuransa na yau da kullum. Ko kuma da badomin koki ta zama mace mai bi sau-da-kafa ga maigidanta ba da maigidanta bai yi suna aka san shi ba, a jiya da yau.

Kenan da mata a yau za su yi koyi da halin koki wajen iya shimfida tubalin gina zamantakewa, da sun huta da halin da wasu suke ciki na nukura da ni-'yasun da suka sami kansu a yau.

4.0mace a Rubutaccen Habarce

Shi kuwa rubutaccen habarce ya fito da hallayar 'ya mace a fili yadda kusan kowa ke iya gani ba tare da danjagora ba.Idan aka dubi mataye irinsu Wakale a littafin *Nagari Na Kowa* da Zainabu a *Jiki Magayi* da Amina a littafin *Shehu Umar*da sauransu.

Idan aka dauki wakale kawai za a iya cewa ta isa zama tubalin gina rayuwar 'ya mace. Misali:

> *A Danganawa an yi wani manomi sunansa Danduna. Ya yi shekara fiye da ashirin tare da matarsa Wakale, babu wanda ya taba jin tsakaninsu. (Abdullahi, 1977)*

Daga yadda bayani ya bayyana daga littafin za a fahimci cewa lallai Wakale ta isa tubali na gina al'umma, domin an nuna cewa kusan fiye da shekara ashirin babu wanda ya taba jin tsakaninsu, kenan idan har mace ta iya zamantakewa da miji har tsawon wadannan shekaru ai sam-barka domin ta cancanci zama tubalin gina rayuwar abokin zamantakewa.

Zama cikin wannan hali na yau akwai, gobe babu, bai dame su ba.Gaskiya ne sun rasa wadatar dukiya amma suna da ta zuciya,saboda haka suna jin dadin zama. Abin da ya fi ban sha'awa game da wadannan mutane shi ne irin yadda suke zaune. Ubangiji shi kan hada jinin mutane. Kowa kuwa yana fatar ya sami abokin zama wanda sonsu da kinsu da bukatarsu

da ra'ayinsu da burinsu suka zama ɗaya. Idan akwai asirin zama tsakanin mata da miji waɗannan mutane sun same shi . Tun sa'ad da suka fara zama tare yau fiye da shekara ashirin ke nan babu wanda ya taɓa ji, babu wanda ya taɓa gani. Dalili wannan kuwa shi ne saboda sun yarda da cewa haƙuri da abokin zama shi kan sa a ci ribar zama tare.....(Abdullahi, 1977)

Idan an lura da rawar da Wakale ta taka wajen iya allonta, dangane da zamantakewa tsakaninta da maigidanta, za a fahimci cewa lallai ta isa zama ganɗo wadda take iya kare duk wani abu da zai gurɓata rayuwar abokin zama, sannan kuma ta iya gina tubalin da zata kyautata rayuwar al'umma domin ai ta yi an gani wajen gina rayuwar ɗan da suka haifa.

Daga tubalin da Wakale ta gina ne aka sami ɗa mai nagarta wanda shi ma ya taimaka wajen gina rayuwar wasu, tun daga farkon habarcen har zuwa ƙarshe.Kenan Wakale ta zama tauraruwa abar koyi ga sauran mata wajen inganta rayuwar al'umma; gina rayuwa tana farawa ne daga abin da mace ta haifa, wanda shi kuma ana sa rai idan ya girma ya gina rayuwar wasu.Wannan ya nuna mace ke shimfiɗa tubalin gina al'adar rayuwar al'umma.

Haka idan an dubi Zainabu a littafin*Jiki Magayi* wanda Zainabu ta haƙura da abin da iyayenta suka gindaya mata, na ta auri malam shehu, kuma ta yarda domin ta zama abin koyi ga sauran mata, wajen nuna biyayya ga iyayenta.

5.0 Mace a Rubutacciyar Waka

Haka waƙa nan ma an hango mace a mahangar al'ada, musamman yadda waƙar take ganin cewa mace jigo ce a mahangar al'umma wadda take kusan ɗaukar komai na al'adar al'umma, domin a waƙa ne ake fito da kusan komai na al'ada musamman wanda ya shafi mace, haka ta sanya wannan muƙala kawo misalai na waƙa waɗanda suke da alaƙa da mace. Misali waƙa daga bakin Malama Mairamu:

'Yan uwa mata sai ku motsa ku ji,
Zan gargaɗe ku a kan tsabta.

Ku lura da duk abin da nace,
Ku gyara inda nay yi ɓata.

Wanka , wanki da share gida,
Su ne manya a wurin tsabta.

Ko cikin manya da babba kuma,
Haka ma a cikin sha'anin tsabta.

Wanka dai kowa ya san shi,
Shi ne babba a wurin tsabta.

Kulliyomin sai ki yiwo shi uku,
Safe, rana da yamma duk tsabta.

Sa'an nan wanki na kayan gida,
Da tufa su ma su san tsabta.
Kar ki bar kwanoni duk daudɗa,
Ko da sauran abinci ba tsabta.
(Gaskiya ta fi kwabo, 23, mayu, 1958)

Daga abin da wakar ta bayyana tana nuna yadda mace ya kamata ta kasance mai kula da tsaftace jiki da muhalli, sannan kuma ta kara cewa tsaftar ma a kula da ita kusan ko yaushe. Wannan duk tana magana ne a kan mace da ta zama mai inganta rayuwar zamantakewar abokin zama, domin wani lokaci rashin tsafta na haifar da rushe tubalin da aka gina al'adar zaman iyali da ita.

Haka kuma malama Delu Uwargidan Malam Yusufu Sufi Funtuwa Bampai, Kano:[165]ta sake cewa wani abu wajen gina 'ya mace a mahangar al'ada, a inda ta kara bayyana yadda tubulin ya kamata ya sami inganci sai ta ce:

Kuma yin biyayya Gun miji alfanu ce,
Kuma girmamashi Da yi abin daya ce maki,
Su ne ake so gun ki mai yin aure.

Kuma ba musu ko, Kankani ki bari duka,
Haka nan hushi, Da abin daya saki duk,
Ke dai ki yi shi saboda girmama aure.

Sannan ki yo hakuri, A kowane lokaci,
In kin rike haka, Kin bi hanyar gaskiya,
Kuma ba ki tozarta a domin aure.

Mata ma'aura masu, 'ya ya ga batu,
Allah Ta'ala jallah, Shi ya fada haka,
'ya yammu baiwa ce a domin aure.
(Gaskiya ta fi kwabo, Afrilu, 1964)

Kuma zan jawabi, Dan gajere gun ku duk,
Na gargade ku, Maza da mata duk muzo,
Domin mu girmama yin shi haddin aure.

Har ila yau, wannan waka ita ma ta kara hango wani matakin da mace take kara fito wasu muhimman halaye da mace ke nuni da sauran al'umma ta ta yi koyi, musamman mata. Idan an dubi wakar ta fara kira da wasu manyan halaye da kuma dabi'u da a yi koyi da su.

Haka kuma wakar ta koma da jawo hankali wajen kiyaye lafazi da kuma girmama abokin zama, sannan kuma ta nuna sakamakon hakuri da muhimmancin yara domin su ne manyan gobe. Misali a inda yake cewa:

Sannan ki yo hakuri, A kowane lokaci,
In kin rike haka, Kin bi hanyar gaskiya,
Kuma ba ki tozarta a domin aure.

Mata ma'aura masu, 'ya ya ga batu,
Allah Ta'ala jallah, Shi ya fada haka,
'ya yammu baiwa ce a domin aure.

A ƙarshe sai ta rufe waƙar da yin gargaɗi da cewa lallai zama iyali, a kula da shi domin haka shi ne bin gaskiya da kyautata zamantake a tsakanin al'umma. Wannan ya nuna kenan mahangar ta bayyana yadda mace take hango al'adar zamantakewa mai nagarta, da kuma yadda ake samun ci gaban al'umma, sannan musarwa wajen koyi da wasu halaye masu nagarta.

6.0 Kammalawa

Daga bayanin da ya gabata za a fahimci cewa mace na iya zama wata gandɔ mai kare al'umma daga gurbata, sannan kuma duk da haka tana iya zama jigo mai shayar da tarbiyya mai inganci ga al'ummar da ta rayu a ciki. Daga lungunan da aka hango mace a al'adar Hausawa babu wani mahalli da aka hango wanda mace ba ta saita tunanin al'adar wannan al'umma ba, tun daga habarce na baka har zuwa rubutacce da kuma sauran nau'o'in. Domin mahangar ta soma da nuna yadda ake fara tarbiyya tun daga harshe, wanda shi ne yake kusan ɗauke da wasu sassan tarbiyya, sannan mahangarta baje-hajarta da yin nuni da koyo da koyarwa musamman tun daga tsumman goyo har zuwa yadda ake huldɑ da abokin zama kamar yadda wakale da ƙoƙi suka nuna. Saboda haka wannan mahanga bakandamiya ce wadda bayan hange kuma tana nuna wa 'ya mace yadda ake tarbiyyar al'umma, musamman idan ta kai yanayin budurci. Haka kuma tana tanadar kusan duk wani nau'in yanayi na tarbiyya yadda ake cusa wa al'umma, kai al'umma tudun-muntsira a rayuwa.

A ƙarshe sai ta rufe waƙar da yin gargaɗi da cewa lallai zama iyali, a kula da shi domin haka shi ne bin gaskiya da kyautata zamantake a tsakanin al'umma. Wannan ya nuna kenan mahangar ta bayyana yadda mace take hango al'adar zamantakewa mai nagarta, da kuma yadda ake samun ci gaban al'umma, sannan :nusarwa wajen koyi da wasu halaye masu nagarta.

6.0 Kammalawa

Daga bayanin da ya gabata za a fahimci cewa mace na iya zama wata ganɗo mai kare al'umma daga gurbata, sannan kuma duk da haka tana iya zama jigo mai shayar da tarbiyya mai inganci ga al'ummar da ta rayu a ciki. Daga lungunan da aka hango mace a al'adar Hausawa babu wani mahalli da aka hango wanda mace ba ta saita tunanin al'adar wannan al'umma ba, tun daga habarce na baka har zuwa rubutacce da kuma sauran nau'o'in. Domin mahangar ta soma da nuna yadda ake fara tarbiyya tun daga harshe, wanda shi ne yake kusan ɗauke da wasu sassan tarbiyya, sannan mahangarta baje-hajarta da yin nuni da koyo da koyarwa musamman tun daga tsumman goyo har zuwa yadda ake huldа da abokin zama kamar yadda wakale da ƙoƙi suka nuna. Saboda haka wannan mahanga bakandamiya ce wadda bayan hange kuma tana nuna wa 'ya mace yadda ake tarbiyyar al'umma, musamman idan ta kai yanayin budurci. Haka kuma tana tanadar kusan duk wani nau'in yanayi na tarbiyya yadda ake cusa wa al'umma, kai al'umma tudun-muntsira a rayuwa.

Manazarta

Al-Hashimi, A.M. (2013) . *The Ideal Muslimah* : Riyadh Kindom Saudi Arabia. Islamic Publishing House, 2nd Edition

Ahmad, U.B. (1985).*A Taxonomy of Hausa Drama.* Ahmadu Bello University Press, Zaria.

Ahmad, S. (1990). ''Sake Leka Rabe-Raben Wasannin Kwaikwayon Hausa,''. Mukalar da aka gabatar don neman digiri na biyu, Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello Zaria.

Ahmad, S.B. (1997). *Narrator as Interpreter Stability and Variation in Hausa Tales.* Rudiger koppe Verlag Koln .

Bichi, A.Y. (1979). '' Cultural Reflection in Hausa Folklore''. in Yahaya, I.Y.etal (eds) *Harsunan Nijeriya* Vol. IX. Kano: Centre for the Study of Nigerian Languages, Bayero University, Nigeria.

Dunfawa, A.A. (2004) . Matsayin Mace Ga Idon 'Yan Boko da Gargajiyar Bahaushe.*Dundaye Journal of Hausa studies*, the Department of Nigerian Languages, Vol. 1. No.1 UDU Sokoto.

Dangambo, A. (2008) . *Rabe-Raben Adabin Hausa*: Kano Amana Publishers Limited.

Furniss, G. (1995). *Poetry Prose and Popular Culture in Hausa.*Edinburgh University Press.

Gusau, S.M. (2000) *Tatsuniya A Rubuce*: Gidan Dabino Publishers. Kano-Nigeria.

Gusau, S.M. (2006).''Tatsuniya (Gatanan): Sigoginta da Hikimominta''. Algaita Journal of Current Research in Hausa Studies: Department of Nigerian Languages No. 4 Vol.1 Bayero University, Kano.

Sekula,H. (2008). ''Family and Gender Relationships in Two Nigerian Drama Texts,'' *Zaria Journal of Liberal Arts*: Faculty of Arts, Vol.2, No1, Ahmadu Bello University, Zaria.

Jamal, A.B. (2005) . *The Position of Women.*Islamic Dawal Centre

Junaidu, da 'Yar aduwa (2007) .Harshe da Adabin Hausa a Kammale.Spectrum Books Limited Ibadan.

Kofoworola, (1987). *Hausa Performance Arts and Music.*Nigerian Magazine, Lagos.

Laurie, A.B. (1998). *Women State and Political Liberalisation:* New York: Colombia university Press.

Malumfashi, A.I. (1985). ''Bori: Addini ko Wasa''. Mukalar da aka gabatar a Makon Hausa, Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello Zaria.

Robinson, C. (1913). *Hausa Dictionary:* Third Edition Revised and Enlarged, Cambridge at The University, Press.

Garba, R. (2009).'' Mace a Rubutaccen Wasan Kwaikwayo'':Zaria.*Uwar Gulma da Kulba na barna:* Harshe Journal of African Language Vol 3. Department of African Languages, Ahmadu Bello university, Zaria.

Tahir, R.M. (2012) ''The Position of Women In Habarcen Hausa'': Kano. Paper Presented *at 7th conference Literature of Northern Nigeria*, Departmentof English, Bayero University.

Tahir,R.M. (2013) .'' Wasan 'Yartsana a Matsayin Tubalin Gina Tarbiyya a Kasar Hausa: Katsina. Mukalar da aka Gabatar a Taron Kasa kan Tabarbarewar Al'adun Hausawa a Yau'', Jami'ar Umaru Musa 'Yar'aduwa, Katsina. Ranar 25th -26 Ga watan Yuni, 2013.

Skinner, N. (1969) .*Hausa Tales and Traditions.* Vol I Frank Cass and Company.

Skinner, N. (1980) .*Anthology of Hausa Literature.* N.N.P.C. Zaria.

Umar, M.B. (1987), ''Tarbiyya A Bahaushiyar Al'ada'', Maƙalar da aka gabatar a Babban taron ƙara wa juna Ilimi kan Harshe da Adabi da al'adu, CibiyarNazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano

Yahaya, I.Y. (1978). ''Nazari Kan Yanayin Wasan Kwaikwayon Hausa'', Paper presented in first International Conference on Language, Literature and Culture.Bayero University, Kano.

Yahaya, I.Y. (1974).*Labarun Gargajiya* 1.Oxford University Press.

Yahaya, I. Y. (1971) ." The style and Content of a Hausa Tale" a *Harsunan Nijeriya.* Kundi na ix .Jamia'r Bayero Kano.